# Bayanai game da baƙi da kuma biza ta wadanda aka ci wa zarafi ta hanyar lalata ko kuma rikici tsakaninsu da wasu

Ana shawartar ɗalibai daga ƙasashen ƙetare da manazarta da ke da tambayoyi game da shige da fice da kuma takardar neman izinin shiga kasa wato biza da su nemi tallafi na lauyoyi da ke da masaniya game da harkokin baƙi da shige da fice. Wannan takardar za ta taimaka wajen yin bayani game da wasu ɓangaori ne na doka amma kuma hakan ba ya na nufin ta maye gurbin shawara ce ta fannin shari'a ba.

**Ni wanda aka ci wa zarafi ne, shin matsayina baƙo zai iya shafar damata ta samun wasu bayanai a cikin jami'a?**

A'a.  Doka ta baiwa ɗalibai da ma'aikata wanda aka ci wa zarafi ta hanyar lalata ko kuma fito na fito 'yanci iri ɗaya ƙarƙashin dokar nan mai taken IX ta shekarar 1972 ta harkokin ilimi da aka yi wa gyaran fuska (Title IX) da kuma dokar nan ta cin zarafin mata (VAWA), ba tare da la'akari da matsayinsu na baƙi ko kuma irin bizar da suke da ita ba.

Za a iya samun bayanai game da harkar kiwon lafiya a cikin makaranta da batu na bada shawarwari da kuma wuraren kwanan ɗalibai da ake da su a: https://www.tntech.edu/healthservices/

Za a iya samun bayanai game da ɗabi'ar ɗalibai a: https://www.tntech.edu/policies/

Kwalejin ba za ta yi ramuwar gayya ko kuma yin mu'amala da kai a wani tsari da zai kasance daban da na sauran sauran jama'a ba don ka sanar da ita game da wani laifi da aka aikata.

**Zan iya shigar da ƙara kotu a matsayina na baƙon haure da ke da rijista ko akasin haka?**

E. Za a iya samun bayanai game da yanayin cin zarafi ta hanyar lalata da rikici na gida da faɗa tsakanin masoya da kuma irin masu yin bibiko din nan a rahoton shekara-shekara na harkar tsaro: https://www.tntech.edu/police/annual-security-report

Za a iya aikewa da tambayoyi game da batun shigar da ƙara ga:

Zeva Edmondson, Title IX Office
1 William L. Jones Dr., Derryberry Hall 256, Cookeville, TN 38505
931-372-3112
https://www.tntech.edu/titleIX
zedmondson@tntech.edu

**Shin akwai wani keɓantaccen matsayi na biza ga baƙin da aka ci wa zarafi?**

E. Ga wadanda aka yi wa cin zarafi ta hanyar lalata da rikici na gida da faɗa tsakanin masoya da kuma irin wanda ake wa bibiko akwai  zabi na biza ciki kuwa irin biza din nan ta U da T. Domin samun karin bayani sai a tuntubi lauyoyi da ke da ɓwarewa kan harkar baƙi da shige da fice.

| Biya ta U | Biza ta T |
|---|---|
| Ga wadanda aka ci wa zarafi sakamakon wani laifi da aka aikata ciki kuwa har da cin zarafi ta hanyar lalata da rikici na gida da fyaɗe da sauran laifuka<br>-Dole ne wanda aka ci wa zarafin ko wanda ya shigar da maganar ya kasance za cika ƙa'ida ta wanda aka aikatawa laifi kuma ya kasance zai iya taimakawa wajen gudanar da bincike ko ma gurfanar da wanda ya aikata laifin gaban kotu.<br>-Zai kasance ne na tsawon shekaru huɗu kawai<br>-Domin samun ƙarin bayani, tuntuɓi lauyan da ya ƙware wajen harkokin baƙi ko shige da fice sannan a duba:<br><br>http://www.uscis.gov/humanitarian/victims-human-trafficking-other-crimes/victims-criminal-activity-u-nonimmigrant-status/victims-criminal-activity-u-nonimmigrant-status | Ga mutanen da aka yi safararsu<br>-Dole ne su amince da wasu abubuwa da jami'an tsaro za su buƙata daga wajensu don samun hadin kai wajen gudanar da bincike  ko kuma gurfanar da wanda suka aikata safarar mutane gaban kotu (sai dai kuma in ba za su iya taimaka wa ba saboda halin damuwa da suka shiga), kuma dole ne su bada tabbacin cewar wanda aka yi safarar din zai shiga wani hali in an iza ƙeyarsa don ficewa daga Amirka<br>-Zai kasance ne na tsawon shekaru huɗu kawai<br>-Domin samun ƙarin bayani, tuntuɓi lauyan da ya ƙware wajen harkokin baƙi ko shige da fice sannan a duba:<br><br>http://www.uscis.gov/humanitarian/victims-human-trafficking-other-crimes/victims-human-trafficking-t-nonimmigrant-status |

SUNY The State University of New York

**Shin akwai wani ofishi a cikin makarantar da zan samu ƙarin bayani?**

,
, ,

Ofishin da ke kula da ɗalibai da manazarta na ƙasashen waje zai iya bada bayanai masu muhimmanci game da matsayin baƙi. Idan ana buƙatar yin tambaya game da sauya matsayin biza ko kuma zaɓi game da batun shari'a da ba ya cikin cikin tsarin bizar F-1 da J-1 ta dalibai ko biza ta yin aiki to sai a tuntuɓi ƙwararren lauya kan harkokin baƙi ko shige da fice.

| Zaɓi na biza | |
|---|---|
| Matsayin F-1 da J-1 na dalibai<br>• Amincewa da zaɓi na ragin yawan kwasa-kwasai na karatu saboda rashin lafiya daga likita ko kuma masanin halayyar ɗan Adam<br>• Zaɓi na barin karatu ko kuma abinda ka iya biyo baya<br>• Bayani game da komawa karatu a wani lokaci nan gaba idan har ɗalibi ya zaɓi barin karatu<br>• Zaɓi da kuma abinda ka iya biyo baya ga iyalai da suka yi rakiya<br>• Bayanai game da zaɓin da ake da shi na sauya matsayin biza.<br>• Bayanai game da biza ta T da U. (Turawa zuwa ga lauyan da ya ƙware kan harkoki na baƙi)<br>• Turawa zuwa ga ƙwararren lauya | H-1B, O-1, E-3, or TN na ma'aikata<br>• Zaɓi na daukar hutu daga wajen aiki da kuma abinda ka iya faruwa ga matsayinka na bako<br>• Zaɓi da kuma abinda ka iya faruwa ga iyalai da suka yi rakiya<br>• Bayanai game da zaɓin da ake da shi na sauya matsayin biza. Turawa zuwa ga lauyan da ya ƙware kan harkokin baƙi<br>• Bayani game da Biza ta U da T. (Turawa zuwa ga lauyan da ya ƙware kan harkokin baƙi)<br>• Turawa zuwa ga lauyan da ya ƙware kan harkokin baƙi<br>• Lokacin da za a samu takarda izinin zama (ba a amince da takardar zama ta Green Card ba)<br>• Tasiri game da barin aikinka - buƙatar neman takardar izinin zama da aka ɗauki nauyi;<br>• Turawa zuwa ga ƙwararren lauya |

**Menene wani shige da fice lauya da kuma menene suka yi?**

Lauyoyi masu aiki kan harkokin baƙi da shige da fice lauyoyi ne da ke da suke da lasisi kuma suka ƙware a fannin doka da ya danganci baƙi da shige da fice. Su na yin aiki a matsayin lauyoyi na ƙaki kuma za su iya wakiltarsu a hukumomin da ke kula da ƙaki ciki kuwa har da kotu da kuma neman haƙƙi na abubuwan da suka kamata baƙi za su amfana da su. Irin wannan lauya kan iya bada shawara kana ya tattauna zaɓin da baki ke da su. Kamar sauran lauyoyi, lauyoyin da suka ƙware wajen harkokin da ke da nasaba da baƙi na aiki ne bisa dokoki da ƙa'idoji na aikin lauya da aka gindaya kuma ba sa gaya kowa irin zantawar da suka yi da wanɗanda suke wakilta.

**Ina zan samu lauya da ya ƙware kan harkokin baƙi?**

| | |
|---|---|
| Bada takardar zama ɗan Amirka da harkokin baƙi (USCIS) wanda wani bangare na sashin harkokin tsaron cikin gida (DHS) ya fidda shafuka biyu na intanet don taimakawa mutane su samu lauyoyin da za su wakilcesu kyauta ko kuma a kan kuɗin da bai taka kara ya karya ba:<br><br>USCIS: Samu Taimako a Shafin Intanet na Yankiku | <br><br><br>USCIS: Samu Shafin Intanet da ya Danganci Harkokin Shari'a |
| Hukumar da kula da ɗaukaka kara kan harkokin baƙi (BIA) na bada jerin sunaye na lauyoyi da ke aiki kan batun baƙi a kowacce jiha musamman wanda ke aiki kyauta ko kuma a farashi mai rahusa. | |
| Kungiyar Lauyoyin Amirka da suka ƙware kan harkokin baƙi (AILA) kan bada bayanai a shafukan intanet da za su taimaka wa ɗalibai da manazarta wajen samun lauyan da ya ƙware kan harkoin baƙi. | |
| Kungiyar Lauyoyin Amirka ma na bada bayanai game da samun taimako na shari'a a jihohi. | |